Da wani mutum zai maka leken asiri ba da izinika ba, sai ka jefe shi da dutse, har ka cire masa ido: ba laifi yin hakan

Daga Abu Huraira -Allah ya yarda da shi- zuwa ga Annabi: "Da wani mutum zai maka leken asiri ba da izinika ba, sai ka jefe shi da dutse, har ka cire masa ido: ba laifi yin hakan

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi ya bada labari cewa da wani zai leka gidan wani ta bayan kofa ko ta saman katanga ko makamanci hakan, sai ya jefe shi da dutse ko ya soke shi da wani karfe a ido, to ba wani abu na zunubi ko na kisasi; Don kuwa shi ya janyowa kansa.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/2989